«لشيطان وشركه وأن أقترف على نفسى سوءاً أو أجُرَّه إلى مسلم»

"Ya Ubangiji ! mahaliccin sammai da kasa, masanin boye da sarari, Ubangijin komai kuma mamallakinsa, ina shaidawa da babu abin bautawa da cancanta sai kai, ina neman tsarinka daga sharrin kaina da kuma sharrin shaidan da abin shirkarsa, da kuma kada in aikatawa kaina mummunan abu ko in kai shi ga wani Musulmi"

«اللهم إنى أصبحت أُشـــهدُك وأشـــهد حملة عرشك وملائكتك وأنبياءك وجميع خلقك بأنك أنت الله لا إله إلا أنت وأن محمدًا عبدك ورسولك»

(أربع مرات)

"Ya Ubangiji ni na wayi gari ina shaida maka ina kuma shaidawa (Mala'iku) masu dauke da al'arshinka da Mala'ikunka da Annabawanka da dukkanin halittunka da cewar kai ne : Allah wanda babu abin bautawa da cancanta sai kai, kuma lalle (Annabi) Muhammad bawanka ne kuma Manzonka ne"

«اللهم إنى أمسيت...»

Da yamma kuma: "Ya Ubangiji ! ni na kai maraice: zuwa karshe," sau hudu) (4)

«لا إله إلا الله وحده لا شريك له. له الملك وله الحمد. وهو على كل شىء قدير»

(مائة مرة) فى الصباح أو المساء)

"Babu abin bautawa da cancanta sai Allah, shi kadai yake ba shi da abokin tarayya, mulki nasa ne kuma godiya tasa ce, kuma shi maiiko ne akan komai."

Sau dari (100), da safe da kuma yamma

«حسبى الله لا إله إلا هو عليه توكلت وهو رب العرش العظيم»

(سبع مرات)

"Allah ya isar mini, babu abin bautawa da cancanta sai shi, a gare shi na dogara, kuma shi ne Ubamgijin Al arshi mai girma."

Sau bakwai (7)

«سبحان الله وبحمده»

(مائة مرة) فى الصباح أو المساء. أو فيهما جميعًا

"Tsarki ya tabbata ga Allah hadi da gode masa"

Sau dari (100), da safe ko da yamma, ko kuma dukkan su

«أستغفر الله وأتوب إليه» (مائة مرة)

"Ina neman gafarar Allah ina tuba zuwa gare shi"

Sau dari (100), da safe ko da yamma, ko kuma dukkan su

**Wannan shi ne gwargwadon abin da ya sawwaka da aka rubuta, ina rokon Allah madaukakin sarki ya anfanar da shi.**

Wanda ya rubuta shi ne: Muhammad dan Salih Al usaimin, 20/1/1418 (Bayan Hijira).

# ZIKIRAI

WADANDA AKE YIN SU DA SAFE DA KUMA YAMMA.

**Muhammad dan Salih Al usaimin, 1418/1/20 (Bayan Hijira).**

ننشر الإسلام بأكثر من 100 لغة

بيان الإسلام
Bayan AL-Islam
تعرف على الإسلام

موسوعة الأحاديث النبوية
HadeethEnc.com
موسوعة تضم ترجمات للأحاديث النبوية وشروحها بعدة لغات

موسوعة القرآن الكريم
QuranEnc.com
موسوعة تضم تفاسير وتراجم موثوقة لمعاني القرآن الكريم

رقم الإيداع: 1445/22366

Ha312-t3

بيان الإسلام
Bayan AL-Islam

مؤلفات فضيلة الشيخ العلامة محمد بن صالح العثيمين رحمه الله تعالى

جمعية خدمة المحتوى الإسلامي باللغات

الأذكار التي تقال صباحا ومساء - **هوسا**

# ZIKIRAI

WADANDA AKE YIN SU DA SAFE DA KUMA YAMMA.

**Muhammad dan Salih Al usaimin, 1418/1/20 (Bayan Hijira).**

بيان الإسلام
Bayan AL-Islam

مؤلفات فضيلة الشيخ العلامة محمد بن صالح العثيمين رحمه الله تعالى

المحتوى الإسلامي



# ZIKIRAI

WADANDA AKE YIN SU DA SAFE DA KUMA YAMMA.

**Muhammad dan Salih Al usaimin, 1418/1/20 (Bayan Hijira).**

بِسْمِ اللَّهِ الرَّحْمَٰنِ الرَّحِيمِ

*Da sunan Allah mai rahama mai jinkai*

﴿ٱللَّهُ لَآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَ ٱلْحَيُّ ٱلْقَيُّومُ ۚ لَا تَأْخُذُهُۥ سِنَةٌ وَلَا نَوْمٌ ۚ لَّهُۥ مَا فِى ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَمَا فِى ٱلْأَرْضِ ۗ مَن ذَا ٱلَّذِى يَشْفَعُ عِندَهُۥٓ إِلَّا بِإِذْنِهِۦ ۚ يَعْلَمُ مَا بَيْنَ أَيْدِيهِمْ وَمَا خَلْفَهُمْ ۖ وَلَا يُحِيطُونَ بِشَىْءٍ مِّنْ عِلْمِهِۦٓ إِلَّا بِمَا شَآءَ ۚ وَسِعَ كُرْسِيُّهُ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ ۖ وَلَا يَـُٔودُهُۥ حِفْظُهُمَا ۚ وَهُوَ ٱلْعَلِىُّ ٱلْعَظِيمُ ﴿٢٥٥﴾﴾ البقرة: 255

﴿Allah shi ne wanda babu abin bautawa da cancanta sai shi, rayayye ne kuma wanda ya tsayu da kansa ne, gyangyadi ba ya kama shi balle barci, shi ke da duk abinda yake a sammai da kassai, babu wanda zai yi ceto a wurinsa sai da izininsa, ya san abinda yake gabansu da kuma bayansu, (su) bayi ba sa sanin wani abu na iliminsa sai abinda ya ga dama su sani, Kursiyunsa ya yalwaci sammai da kassai, kuma ba ya yi masa nauyi kiyaye su, shi madaukaki ne maigirma.﴾

Ayatul Kursiy, Bakara aya ta:255

﴿ءَامَنَ ٱلرَّسُولُ بِمَآ أُنزِلَ إِلَيْهِ مِن رَّبِّهِۦ وَٱلْمُؤْمِنُونَ ۚ كُلٌّ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَمَلَٰٓئِكَتِهِۦ وَكُتُبِهِۦ وَرُسُلِهِۦ لَا نُفَرِّقُ بَيْنَ أَحَدٍ مِّن رُّسُلِهِۦ ۚ وَقَالُوا۟ سَمِعْنَا وَأَطَعْنَا ۖ غُفْرَانَكَ رَبَّنَا وَإِلَيْكَ ٱلْمَصِيرُ ﴿٢٨٥﴾ لَا يُكَلِّفُ ٱللَّهُ نَفْسًا إِلَّا وُسْعَهَا ۚ لَهَا مَا كَسَبَتْ وَعَلَيْهَا مَا ٱكْتَسَبَتْ ۗ رَبَّنَا لَا تُؤَاخِذْنَآ إِن نَّسِينَآ أَوْ أَخْطَأْنَا ۚ رَبَّنَا وَلَا تَحْمِلْ عَلَيْنَآ إِصْرًا كَمَا حَمَلْتَهُۥ عَلَى ٱلَّذِينَ مِن قَبْلِنَا ۚ رَبَّنَا وَلَا تُحَمِّلْنَا مَا لَا طَاقَةَ لَنَا بِهِۦ ۖ وَٱعْفُ عَنَّا وَٱغْفِرْ لَنَا وَٱرْحَمْنَآ ۚ أَنتَ مَوْلَىٰنَا فَٱنصُرْنَا عَلَى ٱلْقَوْمِ ٱلْكَٰفِرِينَ ﴿٢٨٦﴾﴾ البقرة: 285-286.

﴿Manzon Allah yã yi ĩmãni da abin da aka saukar zuwa gare shi daga Ubangijinsa, da mũminai. Kõwanensu yã yi ĩmãni da Allah, da mala'ikunSa, da littattafanSa, da manzanninSa. Bã mu rarrabẽwa a tsakãnin daya daga manzanninSa. Kuma (mũminai) suka ce: "Mun ji kuma mun yi dã'a; (Muna nẽman) gãfararKa, yã Ubangijinmu, kuma zuwa a gare Ka makõma take "
Allah ba ya dorawa rai sai abinda za ta iya, tana da (ladan) abin da ta aikata, kuma tana da (ukubar laifin) da ta aikata. Ya Ubangijinmu kada ka kamamu idan muka manta ko kuskure. Ya Ubangijinmu kada ka dora mana nauyi kamar yadda ka dora shi ga wadanda suka zo kafin mu. Ya Ubangijinmu kuma kada ka dora mana abinda ba za mu iya ba, ka yi mana afuwa ka gafarta mana, kai ne majibintin al'amuran mu, ka taimaka mana akan mutanan da suke kafirai.﴾

Bakara, aya ta: 285- 286.

﴿قُلْ هُوَ ٱللَّهُ أَحَدٌ ﴿١﴾﴾ الإخلاص: 1.

﴿Ka ce: "Shi ne Allah Makadaĩci."﴾

﴿قُلْ أَعُوذُ بِرَبِّ ٱلْفَلَقِ ﴿١﴾﴾ الفلق: 1.

﴿Ka ce "ina neman tsari daga Ubangijin safiya."﴾

﴿قُلْ أَعُوذُ بِرَبِّ ٱلنَّاسِ ﴿١﴾﴾ الناس: 1.

﴿Ka ce "ina neman tsari daga Ubangijin mutane."﴾

cikakkakkiyar surar ake karantawa, kafa uku (3)... (السورة كاملة ثلاث مرات)

«أعوذ بكلمات الله التامات من شر ما خلق» (ثلاث مرات)

"Ina neman tsari daga kalmomin Allah cikakku daga sharrin abinda ya halitta" Sau uku (3)

«بسم الله الذي لا يضر مع اسمه شيء في الأرض ولا في السماء وهو السميع العليم»
(ثلاث مرات)

"Da sunan Allah, wanda babu wani abu mai cutarwa da sunansa a sama ko a kasa . Kuma shi ne Mai ji Masani"

Sau uku (3)

«رضيت بالله ربًّا وبالإسلام دينًا وبمحمد صلى الله عليه وسلم نبيًّا» (ثلاث مرات)

"Na yarda da Allah Ubangiji, da Musulunci addini, kuma Muhammadu tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi annabi" Sau uku (3)

«أصبحنا وأصبح الملك لله والحمد لله لا إله إلا الله وحده لا شريك له. له الملك وله الحمد وهو على كل شيء قدير. رب أسألك خير ما في هذا اليوم وخير ما بعده. وأعوذ بك من شر ما في هذا اليوم ومن شر ما بعده. ربِّ أعوذ بك من الكسل والهرم وسوء الكِبَر. وأعوذ بك من عذاب النار وعذاب القبر»

"Mun wayi gari kuma mulki ya wayi gari na Allah ne , godiya ta tabbata ga Allah, babu abin bautawa da cancanta sai Allah, shi kadai yake, ba shi da abokin tarayya, mulki nasa ne, godiya tasa ce, kuma shi mai iko ne akan komai. Ya Ubangiji ina rokonka alherin wannan yini da alherin dake bayansa, ina kuma neman tsarinka daga sharrin wannan yini da sharrin dake bayan sa. Ya Ubangiji ina neman tsarinka daga kasala da tsufa, da mummunan girma, ina neman tsarinka daga azabar wuta da kuma azabar kabari."

«أمسينا وأمسى الملك لله»

Da yamma kuma sai ya ce: Mun kai yammaci, kuma mulki ya kai yammaci na Allah ne. sai kuma ya ce: "Ya Ubangiji ina rokonka alherin wannan daren.... zuwa karshe, maimakon: Mun wayi gari ya wayi gari. Da kuma (wannan yini)."

«اللهم بك أصبحنا وبك أمسينا وبك نحيا وبك نموت وإليك النشور»

"Ya Allah gareka muka wayi gari, kuma gareka muka yi yammaci, kuma gareka muke rayuwa kuma gareka muke mutuwa, kuma gareka Makoma take."

«اللهم بك أمسينا وبك أصبحنا وبك نموت وبك نحيا وإليك المصير»

"Da yamma kuma sai ya ce: Ya Ubangiji gareka muke yammaci , kuma gareka muka wayi gari, kuma gareka muke mutuwa, kuma gareka muke komawa"

«اللهم ما أصبح بي من نعمة أو بأحد من خلقك فمنك وحدك لا شريك لك فلك الحمد ولك الشكر»

"Ya Ubangiji duk abinda ya wayi gari a gareni na ni'ima ko ga wani cikin halittarka to daga gareka ne, kai kadai, baka da abokin tarayya, yabo naka ne kuma godiya taka ce"

Da yamma kuma sai ya ce:

«ما أمسى بي» ...

"Abinda ya yi yammaci a gare ni..."

«اللهم إني أسألك العافية في الدنيا والآخرة. اللهم إني أسألك العفو والعافية في ديني ودنياي وأهلي ومالي. اللهم استر عوراتي وآمن روعاتي. اللهم احفظني مِن بين يديَّ ومِن خلفي وعن يميني وعن شمالي ومن فوقي. وأعوذ بعظمتك أن أغتال من تحتي»

"Ya Ubangiji ni ina rokonka yafiya anan duniya da kuma lahira, Ya Ubangiji ni ina rokonka afuwa da yafiya a addinina da duniyata da iyalina da kuma dukiyata, Ya Ubangiji ka suturta al'aurata, ka amintar da tsorona. Ya Ubangiji ka tsare ni ta gabana da ta bayana, ta damata da ta haguna da kuma ta samana, ina kuma neman tsari a da buwayarka kada a halakani ta kasa ta."

«اللهم أنت ربي لا إله إلا أنت. خلقتني وأنا عبدك. وأنا على عهدك ووعدك ما استطعت. أعوذ بك من شر ما صنعت. أبوء لك بنعمتك علي. وأبوء بذنبي. فاغفر لي. فإنه لا يغفر الذنوب إلا أنت»

"Ya Allah ! kai ne Ubangiji na, babu abin bautawa da cancanta sai kai, kai ka halicceni ni bawanka ne, ni kuma ina kan al'kawarinka gwargwadon iko, ina neman tsarinka daga sharrin abinda na aikata, ina tabbatar da ni'imarka a gare ni, ina tabbatarda zunubi na, ka gafarta mini, domin babu mai gafarta zunubai sai kai"

«اللهم فاطر السماوات والأرض. عالم الغيب والشهادة. ربَّ كل شيء ومليكه. أشهد أن لا إله إلا أنت. أعوذ بك من شر نفسي ومن شر